Ya kamata kuma mu yi fariya da cewa ko da shike mun fuskanci wassu mawuyacin wahaloli duk da haka kasar nan tamu ta sami ci gaba kan harkokin ilmi, tattalin arzikin kasa da kyautata yanayin zaman duniyar al'umma cikin shekarun nan goma da suka wuce. Alal ga misali, ma'amalar cinikinmu da kasashen waje ya karu da fam miliyan £315 a cikin shakaran 1959 zuwa fam miliyan £629 a cikin shekaran 1969. A cikin shekaran 1959 mun sayar wa kasahen waje man fetur da ba'a tatse ba kusan akalla rabin miliyan ton ne. A cikin shekaran 1969 ya kai ton miliyan 27, sailin nan kuma a cikin wannan shekara ya wuce ton miliyan 50. A cikin shekarun baya kuma kayayyakin da ake kerawa a masana'antunmu ya karu da fiye da kashi dari uku bisa kashi dari. An ribanya yawan daliban da ake daukawa a makarantun sakandare tsakanin shekaran 1959 da 1969. Babban abin sha'awa ne mu yi li'akari da cewa mun fi samun nasara a wadannan fannonin a cikin shekaran 1969 fiye da zamanin da kafin yaki ya tashi.

A yanzu dai mun dauki shararriyar hanya ce wajen samun ci gaba cikin hanzari da kuma zamunta ba tare da ka ce na ce ba. Gwamnati na sane da irin bukatun da al'umma ke da su: wato na samun zaman lafiya da tsaro, kyautata yanayin zaman duniya na yau da kullum da kuma samowa 'yayansu kyakkyawar makoma. Wadannan dai sune manyan abubuwan da ake bukata; wato kalubalan da ke gaban kowace gwamnati, kuma suna bukatan a yi nazari da su da kyakkyawar manufa.

Dukkanmu na sane da cewan duk wani irin muhimmin ci gaba da za'a samu za'a samu ne in har ana cikin kwanciyar hankali da zaman lafiya. Wannan ma shine babban dalilin da ya sa Gwamnatin mulkin soja ta tarayya ta fi bada muhimancin shirye-shiryenta wajen samun ci gaba da kuma maido gwamnati mai bin tafarkin tsarin mulki wacce zata kamala harkokinta bisa ga yadda al'umman kasa ke bukata.

Dukkanmu na bukatan jaruntaka, sanin ya kamata da kuma hakuri wajen shawo kan wahalolin da muke fuskanta wajen maida tafarkin mulkin kasarmu ga fararen hula. Tilas ne a yi ta hanyar da wajen mika ragaman mulkin nan ga zababun wakilan al'umma za'a sami zaman lafiya da kwanciyar hankali irin ta siyasa kuma na zamani jin dindin. Saboda haka tilas ne kada mu gaggauta kan harkoki amma mu yi taka tsantsan.

Na dauki alkawari bayan da muka kare yakin hada kai a watan Janairu cewan zan shaida wa al'umman kasa kafin shekara ya kare irin shiryeshiryen harkokin siyasa da Gwamnatin mulkin soja ke yi. Majalisar Zartaswa ta sojoji ta zartas da kuduri kan wani shiri na manyan ayyukan da zata yi kafin a mika gwamnatin kasa ga fararen hula dauke da sanin alhakin da ya rataya wuyansu. Cikin ginshikan shirin nan guda tara da zai tabbatar da samun zaman lafiya, kwanciyar hankali da ci gaba a kasar nan da:

(*i*) Yi wa rundunar sojojinmu garambawul;

(*ii*) fara aiki da shirin ci gaban kasa da kuma gyara abubuwan da aka bata ko kuma ba'a yi ba a lokacin yaki;

(*iii*) shafe cin rashawa da hanci a zaman mu na duniya;

(*iv*) zartadda kuduri na karshe kan karin kirkiro jihohi;

(*v*) kafa tafarkin da za'a rinka raba gadon haraji;

(*vi*) kirgan yawan al'uman kasa wato *census*;

(*vii*) kafa jam'iyyun siyasa na kasa ga baki dayanta;

(*viii*) shirya yadda za'a tafiyadda babban zaben wakilai na majalisun dokokin kasa da kuma na jihohi.

Zan yi cikakken bayani kan wadannan batu da na ambata a sama da kuma suka fuskanci kasa. Zan sake jaddada cewan tilas ne a yi taka tsantsan da wadannan batutuwan, sailin nan kuma mu yi tunani da irin kuskure da matsaloli wadanda suka aiyana sabili da burin mulkin wassu mutane 'yan kalilan, wanda kuma ya kawo rushewar jamhuriya ta farko.

## *SHIRIN CI GABAN KASA*

Zan yi batu da farko kan shirin ci gaban kasa. Ina mai farin ciki da in shaida muku cewan an gama shirye-shirye na farko. A cikin wannan wata za'a fara amfani da shi bayan da majalisar zartaswa na sojoji ta zartas da kuduri bisa kansa. Daga nan ne kuma za'a bada cikakken bayani. Wannan shirin na kunshe da jarin fam miliyan £1,595 a shekaran 1970-74. Manyan ginshikan wannan shirin guda biyar ne wadanda kuma manufa shine na maida Nigeria:

(*i*) hadaddiya, karfaffawa kuma ba mai dangana kan wassu kasashe ba;

(*ii*) a sami tattalin arzikin kasa mai amfani;

(*iii*) a sami kasa mai albarkan gona.

*iv*) kasa mai albarka da kuma baiwa kowane dan kasa dama daidaiwadaida;

(*v*) kasa 'yantaciya mai kuma bin mulkin dimokuradiyya.

Kudin da za'a kashe wajen kyautata yanayi al'umma ya kai fam miliyan 780.

Mun daura kudurin cikin shekaru hudu masu zuwa mu kara haskaka tattalin arzikin kasar Nijeriya ya zama irin na zamani, sailin nan kuma a kai shi ga matsayin da albarkan kasar mu da ma'aikata don a tabbatar da ci gaban wannan kasa.

Watakila zai zamanto mafi sauki da a yi shirye-shirye fiye da a tafiyad da aikin. In har dai ana bukatan samun cin nasaran wannan shirin tilas ne kowa da kowa a kasar ya tashi tsaye ya bada irin nasa taimakon. Wannan shirin na bukatan a fi bada karfi kan irin ayyukan da ake bukata cikin gaggawa da kuma taimakon al'ummanmu domin mu sami cin nasaran abinda muka sa a gabanmu. Shirin nan na bukatan a kara yawan tsimi da tanadin da muke yi a kasarmu fiye da na zamanin baya.

Abu ne mai muhimmanci a ciwo kan wahalolin tattalin arzikin kasa a 'yankunan da yakin nan ya shafa a lokacin da ake ci gaba da wannan shirin. Haka kuma abu ne mai muhimanci a cikin 'yan shekaru masu zuwa da a kafa ginshikin ci gaban kowane sashe na kasan nan daidaiwadaida kan matsalolin da suka shafi tattalin arzikin kasa da kuma na ilmi. Bai kamata mu bar banbancin ci gaban sassun kasan nan da kuma rashin ci gaban wassu ya yiwa kasar mu barazana.

### *GARAMBAWUL A MA'AIKATAN RUNDUNAR SOJOJI*

Wani muhimmin aiki da ke gaban gwamnatin sojoji shine yin wa rundunar sojoji garambawul. Wani abin farya ne ga rundunar sojojin kasar nan da kuma 'yan sanda kan yadda suka tafiyadda ayyukansu cikin lumana da kuma nasara cikin shekaru ukun nan da suka wuce. Sun sami nasara wajen tsare mutunci da kuma hada kan kasarsu, a kamar yadda aka bukace su da yi bayan rantsuwar da suka dauka. Domin tafiyadda wadannan ayyukan an kara ribanya yawan sojoji. Cikin gaggawa sai aka maida karamar rundunar sojoji da ta fito daga hanyan masu mulkin mallaka ta zama daya daga cikin manyan rundunar sojoji. An kuma kafa rundunar sojojin ruwa da na jiragen sama sun zama masu yaki. A lokacin yakin nan sojojinmu sun kutsa kai cikin dokar daji, sun kuma zauna cikin ramuka ba tare da jin dadi ba. Yaranmu sun sha wannan wuyan cikin hakuri da kuma mazantaka domin tsare mutuncin kasarsu. Mun kuma sani cewan da shike cikin gaggawa mun kara fadada yawan sojojinmu bai

zamanto abu mai sauki ba da a tabbatar da ladabi da kuma biyayyan kowane soja ba a kamar yadda aka san sojojin Nijeriya da shi.

Saboda haka aiki ne a gabanmu na sake yiwa sojojinmu garambawul domin a kara inganta ayyukansu na wajen tsaron cikin gida da kuma tsaro in ko da Allahbashi za'a kawo mana hari daga kasashen waje. A sa'i guda kuma ya kamata mu baiwa sojojinmu abubuwan jin dadi domin su sami daman tafiyadda harkokinsu cikin tsanaki.

Abu ne muhimmi da a kula da lafiyar sojoji masu kuma cikin yanayin farin ciki wajen samun kwanciyar hankali a kasar nan kamar dai na sauran kasashen duniya. Saboda haka wannan aiki da ke gaban mu zai dauki dan lokaci sailin nan kuma za'a badda dimbin kudi wajen gina sabbin barakoki da kuma sayen muhimman kayayyakin aiki da dai makamatansu. Ina fatan za'a cimma yawanci daga cikin wadannan abubuwan da na zana a cikin shirin ci gaban nan na shekara hudu. Mun kuma daura kudurin ganin cewa sojoji zasu ci gaba da bin tafarkin nan da aka san su da shi tun aru-aru wato na tsare mutuncin kasar da hada kai da kuma tsare tafarkin mulkin kasa. Ba za'a yarda a sanya harkokin siyasa ba cikin ayyukan sojoji, ko kuma a yi amfani da su wajen cin ma burin siyasar wassu mutane 'yan kalilan. Ta haka ne kawai za'a iya samun zaman lafiya da kwanciyar hankali.

### *KAUDA CIN HANCI DA RASHAWA*

A yanzu kuma zan yi batu ne game da cin hanci da rashawa a kasar nan tamu. Ya kamata kasar nan tamu ta tashi tsaye wajen inganta yanayin zaman tare. Sabuwar kasa ba za a iya samun ci gaba ba sai dai ko al'ummanta sun iya zaman tare Ba za mu yarda ba da ganin yadda wassu mutane da ke manyan mukamai ke amfani da matsayinsu domin kawai su tara dukiya. Tilas ne a canja ra'ayin zaman tare in har dai ana bukatan samun kyakkyawar sanin ya kamata tsakanin shugabanni da al'umma. Ta haka ne kawai mutane za su sami kwanciyar hankali ta yadda za su bada cikakken taimako wajen samun ci gaba cikin gaggawa.

Wannan ma shi ne dalilin da ya sa Gwamnatin Soja za ta kara ingancin yaki da kauda cin hanci da kuma rashawa a kowane sashe, ko na farar hula ko kuma na sojoji. Za'a dauki wassu sabbin matakai kan dukkan mutanen da aka same su da laifin tara dukiyan da ba na guminsu ba ne su maida su. Za'a kafa hukumomin bincike na musamman da a cikin gaggawa za su kauda cin hanci da rashawa a koina cikin kasar nan. Yaki da kauda cin hanci da rashawa za'a ci gaba da yinsa, sailin nan kuma Gwamnatin Soja za ta san yadda za ta yi maganin nan matsalar kafin a mika ragamar mulki ga fararen hula.

## *KARA KAFA JIHOHI*

Gwamnatin Mulkin Soja ta Tarayya ta san yadda matsaloli suka zama rikitattu kan batun nan na kara kafa jihohi. Majalisar zartaswa na sojoji ta yi nazari da wannan batun kuma cikin tsanaki. Watakila zaku iya tunawa cikin watan Nuwamba na shekaran 1966 a lokacin da na dauki alkawarin cewan zan kirkiro jihohi, na jaddada wassu manufofi wadanda tilas ne za'a yi nazari da su kan batun nan na kafa jihohi. A lokacin na ce:

(*i*) babu wata jiha da zata sami matsayin da zata buwayi gwamnatin tsakiya ba;
(*ii*) kowane jiha zata zama bisa ginshikin jeyogarafiyya;
(*iii*) harkokin mulki su kuma zama masu sauki, harkokin tarihi, sailin nan kuma tilas ne a yi amfani da ra'ayyin al'umma;
(*iv*) kowace jiha za ta sami daman da za ta tafiyadda harkokinta a kamar yadda da suke a karkashin gwamnatin jihohi;
(*v*) zai zamanto muhimmin abu ne kuma a kirkiro jihohin nan a lokaci guda.

Tilas ne kuma a yi amfani da wadannan abubuwa da na zana. Bai kamata a yi amfani da daya matsalar a kuma bar wani ba. Bari in kara baiyana abin da na ke nufi; idan aka yi nazari da girma da yawan mutane da kuma albarkan kasa na yanzu haka, za'a iya raba kasar nan cikin jihohi takwas ko kuma kada su wuce goma sha hudu.

An yi amfani da wadannan manufofi a lokacin da aka kafa jihohi goma sha biyu a watan Mayu shekaran 1967. Na yi shukura da cewan ginshikin kafa jihohin nan goma sha biyu ya sa an sami daidaita harkokin siyasa fiye da yadda da suke a jamhuriya ta farko. Amma kuma na san cewa akwai wassu guna-guni da suka kawo bukatan nan na kara kafa jihohi. Wassu daga cikin bukatun nan na hade ne da batun ci gaba da kuma abubuwan jin dadi daidai-wa-daida. Wassu mutane na jin cewa ya kamata dukkan sassun jihohi su sami wakilci a dukkan ma'aikatun gwamnatin jihohi. Ba zamu iya cimma wadannan bukatun ba tun da shike za'a iya ci gaba da kirkiro jihohi da ba wanda ya san yawansu. A ainihin gaskiya ba za mu iya bada karfi kan batun karin kafa jihohi ba.

Tilas ne mu yi li'akari da cewan daga karshe al'umma ne zasu ga irin abubuwan da muka yi ba kawai ga tarin yawan jihohi da muka kirkiro ba a'a har ma da yadda aka kara ingancin gonaki, yawan masana'antun da aka gina, sabbin makarantu da kuma irin arzikin da mutane suka yi. Domin mu sami wadannan muhimman abubuwan tilas ne mu inganta tattalin arzikin kasar nan. Tuni na yi batu kan wannan a cikin shirinmu na ci gaba.

An kuma shirya shi ne a karkashin ginshikin jihohi goma sha biyu da muke da su a yazu haka. A yanzu muna amfani da albarkan kasarmu a karkashin jihohin nan goma sha biyu dommin tafiyadda harkokin wannan shiri. Bai kamata mu tsaya cif ba. Bamu da lokacin da zamu bata. Na bada gaskiya, sabili da ba wani amfani da za'a samu wajen bada karfi wajen batun kirkiro jihohi kuma, a cikin yanayin da muke ciki. Muna bukatan mu fi ba da karfinmu wajen zamunta al'amura da kuma kyautata yanayin zaman al'ummanmu. Na dauki alkawarin cewa Gwamnatin Mulkin Soja ta Tarayya zata tsare mutuncin dukkan al'umma da kuma abubuwan da ya shafe su a koina cikin kasan nan.

Saboda haka ba nufinmu bane a cikin shekaru hudu masu zuwa da mu dauki wani mataki da zai canja tafarkin jihohin nan goma sha biyu da muke da su a yanzu. Muna bukatan lokaci da zamu zauna kuma harkoki su koma kamar na da bayan wahalolin yaki da aka samu mu kuma fuskanci ayyukan nan na sake ginin kasa bayan yaki. Muna zaune ne dai a kasa mai albarka. Zamu kuma sake yin nazari da al'amura bayan lokaci. In muka tabbatar cewa kasa na bukatan a kara kafa jihohi to babu shakka Gwamnatin Soja zata kafa karfin ta mika ragaman mulki ga farar hula da aka zaba.

Ina bukatan daukan wannan dama da in yi wa kasa kashedi kan irin wahalolin da za'a samu in har muka shigadda batun kabilanci cikin al'amuran tafiyadda harkokinmu. Tilas ne kowane dan Nigeria ya sami 'yancin zama ko aiki a koina cikin kasan nan ba tare da nuna banbancin kabilanci ba. Wannan ma shine dalilin da ya sa muka yi yaki mai tsawon gaske domin tabbatarwa da hada kan kasarmu. Tilas ne kada mu kauce hanyar manufofinmu. Bugu da kari kuma tilas ne mutane su sami daman walawa domin a tabbatar da sabon ci gaba daidai-wa-daida kuma cikin gaggawa. Zai zamanto manufar Gwamnatin Tarayya ne nan da shekaru kadan masu zuwa da ta tabbatar da cewan kowane dan Nigeria na da yancin walawa a koina. Ina kira kan shugabanni da kuma mutane a koina cikin kasan nan da su yi wa 'yanuwansu yan Nigeria marhabin ba tare da nuna kabilanci ba, ko kuma jihohin da suka fito.

### *SABON TSARIN TAFARKIN MULKI*

Wani babban aiki kuma shine tsara sabon tafarkin mulki. Ina da nufin kafa wata hukuma nan ba da jimawa ba da za ta tsara sabon tafarkin mulki. A lokacin da wannan hukumar kuma ta kammala ayyukanta, za'a kira taron majalisar wakilai a lokacin da ya cancanta domin ta yi nazari da kowane irin tafarkin tsarin mulki ne ya kamaci wannan kasa. Bani da shakka cikin zuciyana kan cewa irin abubuwan da suka aiyana a zamanin baya zai sa cewan mu bi tafarkin gaskiya shine na ci gaba da bin tsarin

tafarkin mulki irin na tarayya. A koina cikin kasar nan da na ziyarta akan karbe ni da hannu biyu-biyu, maza da mata, samari da tsaffi, kan bukatunsu na zama yan Nigeria daya cikin kwanciyar hankali ba tare da nuna banbancin kabila ko addini ba. Za su bukaci tsarin tafarkin mulki da zai ba su 'yancin daidai-wa-daida. Tilas ne mu yi li'akari mu kuma tsara tafarkin mulki wanda zai kara haskaka wadannan manufofinmu kuma guji irin kuskuren da aka yi a zamanin baya.

### *RABA GADON HARAJI*

Za'a kuma kafa hukumar raba gadon haraji domin samun zaman lafiyar kasa. Wannan kuma zai shafi yadda za'a tafiyadda harkoki tsakanin gwamnatin Tarayya da na Jihohi. Watakila kuma za'a yi wassu 'yan canje-canje kan tafarkin wucin gadi da muke amfani da shi a yanzu haka.

### *KIRGAN YAWAN AL'UMMAN KASA*

A kuma game da batun kirgan yawan al'umman kasa, zaku iya tunawa cewan kirgan yawan al'umman kasa da aka yi na karshe shine a cikin shekara 1963 a lokacin da ake rubuta. An saba a koina cikin kasashen duniya da a kirga yawan al'umman kasa bayan kowane shekara goma, saboda haka a cikin shekaran 1973 za'a sake kirgan yawan mutanen kasan nan. A kuma kamar yadda kuka sani, ana amfani da irin kirgan yawan al'umma kasa wajen shirye-shiryen ci gaban kasa, shirin yin zaben wakilai majalisa da kuma wassu muhimman dalilai. Saboda haka Gwamnatin Soja zata sa a yi kirgan yawan al'umma kafin ta mika ragaman mulki ga farar hula.

### *JAM'IYYUN SIYASA*

Wani muhimmin aiki kuma shine na kafa jam'iyyun siyasa. Bai kamata a koma kan tsohon batun nan na samun jam'iyyun siyasa da suka shafi jihohi kawai ba, ko kuma na 'yan kabila guda. Ina fatan a cikin 'yan shekaru masu zuwa nan gaba 'Yan Nigeria, ta hanyar aiki tare domin samun gawurtatciyar kasa, zasu kafa jam'iyyun siyasa da zai shafi dukkan kasa kuma mai manufa guda. Ta bin irin wannan hanyar ne kawai wajen kafa jam'iyyun siyasa za'a sami cin nasara wajen gina 'yantatciyar kasa kuma mai albarka. In zamu koma irin tafarkin siyasar da aka saba wato na 'yan ku ci ku bamu kafin kasar ta sami cika burinta to babu shakka zamu koma gidan jiya na samun tashin hankali a kulluyomin. Ina bukatan a yanzu haka in tunatadda al'umman kasa cewa dokar mulkin Soja a cikin shekaran 1966 ya soke dukkan jam'iyyun siyasa. In lokaci ya yi zan kafa sabbin jam'iyyun siyasa da manufofinsu ya shafi kasa gabaki dayanta.

*MANUFOFIN HARKOKIN WAJE*

A yanzu kuma zan yi batu akan manufofinmu na kasashen waje A matsalolin da suka shafi kasashen Afirka da duniya baki dayanta, babu yadda za'a yi wa Nigeria in har ma tana bukatan hakan. A lokacin kasar ke fuskantar wassu wahaloli da 'yan zamanin, kowa dai ya ga batun da ke yi a fili.

Mun yi farin ciki da irin taimakon da wassu kasashen Afirka suka ba mu a zamanin da muke cikin yakin nan. Haka kuma irin taimakon da kungiyar hada kan kasashen Afirka ta bayar na da yawan gaske. Ina daukan wannan dama in sake godewa Shugabannin kasashen da ke da wakilci a cikin kungiyar hada kan kasashen Afirka saboda irin taimakon da suka baiwa Nijeriya wanda ma ya sa har ta sami daman shawo kan makiyan ta da basa kaunan ganin hada kai a kasar. Kasashen Afirkan nan a bisa gaskiya sun ga amfanin lailai Nijeriya ta hada kanta domin ma haka shine zai sa kasashen Afirka su hada kan su. Bugu da kari kuma al'umman da ke da jinin Afirka a jikinsu a koina cikin kasashen duniya sun ga cewan hadaddiyar Nijeriya ita ce fatagare su, wanda kuma zai zama ginshiki ne na samowa bakaken fata daraja, da da ake wulakantawa a ko ina. Saboda haka babban aikin da ke gaban mu shine na samowa kasashen Afirka kwanciyar hankali. Zamu yi aiki ba ji ba gani, ba dare ba rana domin kauda mulkin mallaka da nuna al'umanci a kasashen Afirka, kara karfafa hada kan kasashen Afirka da kuma kakkafa kungiyoyin tattalin arzikin kasa na jihohi a Afirka. A kuma bin kaidodin wadannan manufofi tilas ne mu bi tafarkin nan na baiwa kowace kasa 'yancin ta a Afirka. Ba mu da burin fadada kasarmu ko kadan.

A kuma sauran kasashen duniya da ba na Afirka ba, za mu yi aiki tukuru tare da sauran matasan kasashe domin tabbatar da 'yancin kanannan kasashe, sailin nan kuma mu kauda garkuwoyin da aka sanya bisa kan hanyar ci gaban ku cikin gaggawa wato wadanda kasashen da suka ci gaba suka sanya tun ma ba kan harkokin tattalin arzikin kasa da kuma ciniki ba. Zamu kuma la'anci wulakanta rayukan yan adam da kuma shan wuyansu a ko ina cikin kasashen duniya ko kuma danniyar 'yancin kasashen.

Tilas ne a sami ginshin hada kai tsakanin kasashen duniya ta bin fatan alheri wa juna da kuma hada kai cikin lumana. Saboda haka a majalisar dinkin duniya da sauran majalisun duniya zamu ci gaba da neman kauda hanyoyin nan da ke kawo tashin hankali da kuma haskaka al'amuran samun zaman lafiya a ko ina cikin duniya. Mun san cewan manyan kasashen duniya da kuma sauran kasashen duniya da suka ci gaba na da alhaki na musamman wajen inganta harkokin samun zaman lafiya a duniya da

kuma ci gaban matasan kasashe. A game da wannan ya kamata su dauki mataki na musamman a shirin ci gaba na majalisar dinkin duniya a karni na biyu.

Za'a kuma kara fahimtadda manufar nan namu na zaman 'yan barwanmu. Ba abinda zai dami Nijeriya cikin yakin cacan baki da na manufofi. Saboda haka zamu hada kai da dukkan kasashe da ke bukatan hada kai da mu wajen inganta albarkan kasarmu da kuma inganta yanayin zaman al'ummanmu.

*ZABEN ZUWA MAJALISUN DOKOKI DA BABU CUKU-CUKU*

Daga karshe, shine batun zaben falan daya rana daya kuma don balagaggu da babu cuku-cuku don zuwa majalisun dokokinmu; a lokacin da muka yi wa sojojin garambawul, shirya sabon tsarin tafarkin mulki, mu kirga yawan al'ummanmu, mu kauda cin hanci da rashawa a kasar mu, mu kuma sami cin nasara kan sauran wahaloli da na batu kai tun farko, zai zamanto alhakin Gwamnatin Soja ne da ta shirya zaben falan daya rana daya don balagaggu ba tare da wani cuku-cuku ba domin ta sami daman mika ragaman mulki ga zababbiyar gwamnatoci. Tilas ne cikin sanaki ta tafiyadda harkokin babban zaben nan domin a tabbatar da cewan an sami cin nasara. Muna da niyyar aikata wadannan abubuwa a hankali kuma ta hanyar gaskiya ta yadda za'a mika wa farar hula gwamnatoci ta tafarkin da ya kamata.

*SHIRIN YADDA ZA'A KAMMALA WADANNAN AYYUKAN*

'Yanuwana maza da mata, kun san an ce mutum sai Allah, Saboda haka ba zai zamanto daidai ba a ce in kana ma'amala da mutum ka bashi tabbas kan shirye-shiryenka wajen samun nasara kan muhimman matsaloli kuma mawuyata. A farkon shekaran 1970 mun yi fatan cewan shirin nan da majalisar zartaswa na sojoji ta zartas na shirin shekara biyu domin maida kasar ga hannayen mulkin farar hula a cikin shekaran 1969. Abin bakin ciki shine taurin kai da yakin da 'yan tawaye suka tayar sai suka bata mana shirinmu.

Muna fatan cewan kwanakin siradi sun wuce. Amma kuma wahalolin yakin nan har yanzu suna nan—akwai gonaki, masana'antu da kuma garuruwan da aka bata a 'yakin da aka yi, hanyoyin motoci da gadaje, makarantu da kuma ba'a kulawa da yanayin jin dadin al'umma kamar yadda aka saba, don mun bada karfinmu kan tsare mutuncin kan kasar mu da kuma hada kai. Alhaki ne kan Gwamnatin Soja da ta kauda duk wasu wahaloli da yakin nan ya kawo. Muna fatan mu sami nasara kan wannan matsalar nan da shekaru hudu masu zuwa. Zamu kuma sami ci gaba cikin gaggawa a wannan lokacin don mu sami nasara kuma kan muhimman ayyukan nan guda tara da na baiyana.

Domin a sami nasara kan wannan shirin muna bukatan kowa da kowa ya taimaka aiki tukuru kuma tsakani da Allah da kuma irin bajintar da sojoji da kasa ga baki daya ta nuna a lokacin da ake yakin nan. Muna tsammanin a cikin shekaran 1976 zamu gama ayyukan da ke gabanmu kuma mika ragaman mulki ga hannayen farar hula. Zamu gaggauta domin ko zai yiwu mu gama wadannan ayyukan kafin wancan lokacin. Muhimmin abu ne mu yi aiki tare kuma cikin lumana. Babu dama wata kungiya da ba sa kaunan ganin cin nasaranmu su zaci ko zasu kauda hankulan mu daga wadannan muhimman ayyukan. Daga lokaci zuwa lokaci zan rinka baiwa kasa rahoton irin ci gaban da ake samu akan wannan shirin.

Na tabbata zan bada gaskiya na ga sojojinmu domin samun cikakken goyon bayansu a wadannan mawuyatan shekaru da ke kan gabanmu domin mu za mu tadda kasarmu ta yadda sauran kasashen duniya ma zasu bamu darajar da ya cacanta. Na kuma bada gaskiyan cewa kowane na kasar nan zai ji bayanin nan da na yi kuma zasu dauran aniyar yin aiki tukuru domin cin nasaran wannan kasa tamu.

Mun yi nazari da irin matsalolin da ya shafi al'ummanmu ne tun ma ba samari ba a wajen shirya wannan shirin ci gaba. Ina kira kan samarin kasarmu da su tashi tsaye su kuma nuna bajinta da aiki tukuru. Ina kira ma musamman ne kan wadanda ke bukatan zama shugabanni nan gaba. Kuna da alhaki kanku kuma na musamman da zaku aikata domin ganin Nijeriya ta zama muhimmiyar kasa kuma mai kwanciyar hankali. Babban alhaki ne kanmu da kuma sauran kasashen Afirka da mu tashi tsaye domin gina sabuwar kasarmu mai albarka. Allah ka taimakemu.

ALLAH YA KUMA SA A SAMI HADADDIYA KUMA KARFAFFIYAR NIJERIYA.